# Duk wanda ya halarci gawa har akai mata salla yana da kiradi guda,wanda kuma ya halarce ta har aka binneta yana da kiradi biyu,aka ce:menene kiradi biyu?yace:kwatankwacin manyan Duwatsu biyu

an karbo daga Abi Huraira Allah ya yarda dashi an daga hadisin zuwa ga Annabi: "wanda ya halarci Gawa har akai mata salla yana da kiradi guda.wanda kuma ya halarce ta har aka binneta yana da kiradi biyu.sai aka ce: menene kiradi biyu? sai yace: kwatankwacin manyan dutsuna biyu" a wata ruwayar kuma: "mafi kankantarsu kwatankwacin dutsen Uhudu"

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Allah mai madaukakin suna da albarka mai tausasawa ne ga bayinsa, sa`annan yana nufin da ya shimfida musu dalilan yin gafara a garesu, musamman ma lokacin da zasu bar duniya, wadda ta ke ita ce gidan aiki, izuwa gidan da za`a ninke takardun ayyukan su a cikin ta. don hakanan ne ya kwadaitar bisa yin sallar jana`iza da halartar ta, saboda ita sallar neman ceto ne ga mamaci kuma tana kasancewa dalilin samun rahamar Allah. sai ya sanya ladan qiradi ga wanda ya sallace ta, ya kuma sanya wani ladan qiradin ga wanda ya halarci binne ta. wannan wani gwargwado ne daga lada mai girma kuma matsayinsa sananne ne wurin Allah madaukakin saki. yayin da gwargwadon girman wannan lada ya buya ga sahabbai Allah ya kara yarda a gare su- sai Annabi mai tsira da aminci su kara tabbata a gareshi ya kusanto da shi ga kwakwalen su, ta yadda kowane qiradi ya kai girman babban dutse; saboda abinda ke ciki na girma tsayawa akan hakkin dan uwansa musulmi tare da yin addu`ah a gareshi da tunatarwa dangane da makoma da debewa mutanen gidan kewar mamacin su da wanin haka da maslahohi.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee